

**Sunana Shyam, ni dan shekara goma ne.**

**Ni ba mai kiba bane sossai, amma siffata tana da kwarjini!**

**Farkawa daga barci zuwa makaranta abu mai wahala ne a guna.**

**Saboda in da nauyin barci, idan na farka jinake kamar zan fadi.**



**Na ji kanwata Amma tana ta gaggawa.**

**Ni kuma, idanu na sai kara lumshewa suke yayin da nake wanke baki,**

**Da sannu zuciyata sai ta nitsa cikin tunanani,**

**Abubuwa dayawa sai fado min zuciyata suke.**



**Ina ma wuyata tana da tsawo sossai?**

**Kawai da sai in tura rabi makaranta, in bar rabi a gida.**

**Da haka zai yiwu, to ina zan kasance ke nan?**



**Ina ma kafafuna suna da tsawo kamar bishiya?**

**Da ginin makarantarmu ya kasancemin iya gwiwa!**



**Ina ma hannaye na suna da karfi sossai?**

**Da daukan Amma ya zo min cikin sauki!**



**Ina ma komai zai kasance mai laushi wajen taunawa da hakorana?**

**Da na ci abubuwa da yawa!**



**Ina ma ciki na zai kasance babba sossai?**

**Da dukan abokaina sun yi tsalle suna shewa, kai da na zama abin tsokana!**




**Ina ma ina da kunnuwa fala-fala kamar na giwa?**

**Kai da na zam mai jin komai, na kusa da nesa!**



**Ina ma...kawai sai Amma ta zo ta firgita ni da ihu, ta ce**

**"Shiyam, za ka makara fa, tunanin me kake haka?"**



**Sai wuf na dawo cikin hayyacina,**

**Ashe har yanzu ina tsaye ne da abin goge baki a hannuna,**

**Sai na dan yi murmushi, kan abubuwan da na boye cike da tunaninsu.**